# ALLAH YA BADA WANI SHAIDA MARA KUSKURE DA YA TABBATAR DA CEWA FYAUCEWA ZAI AUKU RANAR 21 GA MAYU, 2011.

Allah cikin babban jinkansa ya bada kyakyawan shaida da cewa shekara ta 2011 ce zata zama shekarar fyaucewa wanda ya yi daidai da ranar shari'a da kuma karshen duniya. A tuna cikin Bitrus ta biyu sura 3 a aya ta 8, cikin mahallin da ke jan hankalinmu zuwa ga ruwan tufanan kwanaki Nuhu da kuma zuwa ga hallakaswar wannan duniya a karshen lokaci, ya furta da cewa: **"rana daya a wurin Ubangiji kamar shekara dubu ce, shekara dubu kuma kamar rana daya ne."**

Shekaru da sun wuce mun koya daga Littafi mai Tsarki da cewa ruwan tufana ya auku cikin shekara ta 4,990 kafin zuwan Almasihu. Kwananan kuma mun koya cewa ranar shari'a zai auku cikin shekara ta 2011, shekarar Ubangijinmu. <u>Shekara ta 2011, shekarar Ubangijinmu, yana daidai da shekaru 7,000 bayan shekara ta 4,990 kafin zuwan Almasihu.</u>

Dab da ruwan tufanan, Allaha ya gayawa Nuhu da cewa cikin kwanaki bakwai ruwan tufana zai fara (Farawa sura 7 a aya ta 4 da aya ta 10 zuwa ta 16). Moran harshen littafin Bitrus ta biyu sura 3 a aya ta 8 da ke cewa rana daya kamar shekaru dubu ne, Allah ya more Nuhu, wanda shi mai-wa'azin adalci ne (Bitrus ta biyu sura 2 a aya ta 5) domin ya furta wa "bil'adama cewa suna da kwanaki bakwai ko kuma shekaru 7,000 su tsere wa hallakaswa." Tun da 2011 shekarar Ubangijinmu daidai yake da shekaru 7,000 bayan Nuhu ya yi wa'azin wannan kashedi, Allah ya bawa bil'adama kyakyawan shaida ke nan da cewa ranar shari'a zai auku cikin shekara ta 2011.

Allah ya maimaita wannan magana "rana daya kamar shekara dubu ne" domin ya kara tabbatar mana da cewa Allah ne fa ya kafa wannan, ba da jimawa kuma ba zai sa ta zo ta wuce (Farawa sura 41 ta 32).



<u>**WANI SHAIDA**</u>

Allah cikin jinkansa ya sake bada wani babbar shaida. Yana kamar haka, mun rigaya mun koya cewa daidai lokacin giciye shi ne ranar fari ga Aprilu, allip 33, idan an daidaita shi da kalandar mu na zamani. Ranar farko ga Aprilu, allip 33 shi ne ranar kadai da ya cika dukan abin da Littafi mai Tsarki ke bida, wato kamar kasancewar Ju'mman da ya fado daidai da ranar faska, wanda shi ne ranar da ake giciye Almasihu.

Mun sani kuma, har dai na yar lokaci yanzu da cewa ranar farko na ranar shari'a ya yi daidai da ranar da fyaucewa zai auku, wato, ranar 21 ga Mayu, 2011. Amma kuma an gane cewa daidai kwanaki 722,500 ne ke akwai daga ranar farko ga Aprilu, allip 33 zuwa ranar 21 ga Mayu, 2011. Wannan gaskiyar ya sake bamu wani tabbataciyar shaida, mara kuskure da cewa ranar 21 ga Mayu, 2011 ce ranar fyaucewa da kuma farawar ranar shari'a.

Domin muhimmancin da kuma iya bada mamakin wannan shaida, zamu dauki lokaci mu tayar da ita, da farko dole mu koya da cewa za mu iya tayarwa da dukan tabbaci, yawan kwanaki daga wani lokaci zuwa wani. Domin samun daidai yawan kwananki daga wani lokaci a cikin wani shekara zuwa daidai wannan lokaci cikin shekara na gaba, dole mu gane cewa masu ilimin tauraro tuntuni sun gano da cewa kwanaki 365.2422 ne ke akwai cikin cikakiyar shekara. Shi ya sa a cikin kalandar mu na zamani kwanaki 365 ne ke akwai cikin kowane shekaru uku masu bin juna. Ko da ya ke, kowace shekara ta hudun kwanaki 366 ta ke dauke da su. Ana yi wannan ta wurin kara rana daya cikin watan Feburairu na wannan shekarar.

Don haka, tsakiyar shekaru hudun nan zai zama kwanakin 365.25. Amma .25 ya fiye .2422 girma, don haka ana sauke rana daya daga kalandar kowace shekaru 128 domin a cigaba da daidatuwa.

Don haka, dukan abin da ya kamata mu yi shine mu sauya shekarun da ke tsakanin abubuwan biyu da wannan lamba 365.2422 domin mu san daidai kwanakin da ke tsakanin su. Don haka, daga ranar farko ga Aprilu, allip 33 zuwa ranar farko ga Aprilu, allip 2011, akwai daidai shekaru 2011-33 = 1,978, kowace shekara kuma yana dauke da kwanaki 365.2422. Wannan yana daidai da kwanaki 722,449. Yawan kwanaki kuma daga ranar farko ga Aprilu, allip 2011 zuwa ranar 21 ga Mayu, allip 2011 (a hade, wato da ranar farko da na karshe a hade), kwanaki 51 ne ke akwai. A hada kwanaki 51 da kwanaki 722,449, za a samu daidai kwanaki 722,500 daga ranar farko ga Aprilu, allip 33 zuwa ranar 21 ga Mayu, 2011 a hade.



Wannan lambar yana da matukar muhimmanci a yanzu dai, zamu gan masababin wannan.

<u>**Wasu lambobi a cikin Littafi mai Tsarki suna iya dauke da gaskiya cikin ruhaniya.**</u>

A wasu lokuta Allah yakan more kalamai a hanyar da suke dauke da gaskiya cikin ruhaniya, ko da ya ke ba a safai suke cikin yadda an saba moran kalaman a zahirce ba. Alal misali, kalmar nan "Dan rago" sau da dama akan Almasihu a matsayin dan rago ya ke magana. Kalmar nan "dutse" sau da dama yana magana ne akan "Mulki," "gona" kuma "duniya," "jinni" kuma yana nuna hadayar ran Almasihu, "Urushalima" kuma mulkin Allah. Haka ma, wasu lambobi a cikin Littafi mai Tsarki, wadanda ana rubuta su kamar kalamai, ba dai kamar lambobi ba, suma sau da dama manuna ne ga gaskiya cikin ruhaniya. Zamu dubi lambobi guda biyar da suke misalun wannan, yayinda suke kafa ido ga gaskiya cikin ruhaniya masu muhimmanci. Labobin ke nan 3, 5, 10, 17 da kuma 23.

Lamba 3 yana nuna nufin Allah. Lokacin da Littafi mai Tsarki ya yi magana akan an giciye Almasihu, an bayyana lamba 3 kusan sau 15; giciye 3, manzanni 3 tare da Yesu cikin gona, musun Bitrus sau 3, da sauran su. Duk wadannan bayyanuwar lamba 3 suna nanatawa ne da cewa lallai nufin Allah a giciye Almasihu.

Lamba 5 yana nuna kafara ko kuma fansa (wato, Almasihu ya mutu domin ya biya hakkin zunuban wadanda zai ceta). Ana ganin wannan, alal misali duban rabi (1/2 ko kuma 0.5) na shekel na kudin fansa wanda ya kafa ido ne akan kafara. Fitowa sura 30 a aya ta 15 ya furta cewa:

***"Mai-arziki ba za ya hawas ba, matalauci ba za ya karamta ba, bisa ga rabin shekel, sa'anda suke ba da hadayar Ubangiji, domin kafarar rayukanku."***

An sake kwatanta hoton fansa ta wurin shekels biyar na littafin Lissafi sura 3 a aya ta 47 zuwa ta 48:

***"Sai ka dauki shekel biyar biyar a bakin kowane dayansu; ana lissaftawa bisa ga shekel na wuri mai tsarki (shekel shi ne gerah ashirin); wannan kurdi fa da aka panshi abin da ya dara sai a ba Haruna da ya'yansa."***

Lamba 10 ko 100 (10 sau 10) ko kuma 1,000 (wato 100 sau 10) suna nuna cikawa ne. Alal misali, Littafi mai Tsarki ya yi magana a wasu wurare game da sullala 10 ko kuma raguna 100, ko kuma shekaru,



1,000. Allah ya yi magana akan an daure shaitan har shekaru 1,000 cikin Ruya ta Yohanna sura 20 a aya ta 2 zuwa ta 3. Ko da ya ke, daga sauran sakonai Littafi mai Tsarki mun san cewa an daure shi ne tsakanin allip 33 da allip 1988.

An nuna wadannan shakaru 1,955 da shekaru dubu daya. Littafi mai Tsarki ya yi magana akan daure shi har shekaru 1,000 domin a nuna cewa an daure shi zuwa cikawan shirin Allah, wanda a zahirce lokaci ne mai tsawon shekaru 1,955.

Sau da dama lamba 17 yana nuna Samariya. Alal misali, cikin littafin Irmiya Allah ya kwatanta hallakaswar Yahuda da Urushalima ta hannun sarki Babila wannan ya zama misalin karshen lokaci tazarar ikkilisiya ne wanda a lokacin shaitan, wanda aka yi misalinsa da Sarki Babila, yana hallakadda Urushalima da Yahuda, zai yi mulki cikin ikkilisiyai. Cikin irin wannan mahallin da kamar babu sauran bege an umurce Irmiya ya sayi fili akan adadin shekel na azurfa 17. Allah ya umurce Irmiya da cewa sayan wannan filin akan shekel 17, ya zama hakanan ne akan tabbacin ko kuma kwatancin da ke cewa lokaci na zuwa da Israila zasu sake mallakan Urushalima. Wato, mutane kuma zasu sake shigan sama. Duba Irmiya sura 32 a aya ta 7 zuwa ta 17.

Lamba 23 yana nuna hallakaswa ne. An kwatanta wannan, a kalla, cikin wurare biyu masu muhimmanci a cikin Littafi mai Tsarki. Daya daga cikin wuraren ya yi rubutu akan annoba mai hallakaswa da Allah ya aiko akan Israila domin sun soma bautar alloli mai suna Ba'alpeor. Allah ya rubuta wannan hukunci cikin littafi Lissafi sura 25 a aya ta 9:

***"Wadanda suka mutu da annoba, mutum dubu ashirin da hudu ne."***

Haka ma, Littafi mai Tsarki ya yi magana akan wannan annoban a cikin sabuwar alkawari. Mun karanta wannan cikin Korintiyawa ta fari sura 10 a aya ta 8:

***"Kada mu yi fasikanci kuma, kamar yadda wadansu daga cikinsu suka yi, rana daya kuwa suka fadi, mutum dubu ashirin da uku."***

A lura, Allah ya rubuta hallakaswar 24,000 a cikin tsohuwar alkawari sa'annan 23,000 a cikin sabuwar alkawari. Wannan dai ba sabani bane. Gaba daya mutane 24,000 ne aka hallaka, wadanda daga cikinsu an hallakadda 23,000 cikin rana daya. Wannan yana kara nanata dangantakar wannan lambar da hallakaswa.

Wani nuni kuma na dangantakar wannan lambar 23 da fushin Allah yana samuwa cikin littafin Daniyel sura 8. A can Allah ya yi magana akan wani lokaci (wanda a yanzu mun san cewa ita ce sashe na farko na matsananciyar kunci) mai tsawon kwanaki 2,300 wanda a cikinta shaitan yake mulki dukan ikkilisiyai da kuma cikin duniya yayinda Allah ya soma kawo hallakaswa akan ikkilisiyai, domin ya shirya su da kuma duniya domin ranar shari'a. Mun karanta cikin Daniyel sura 8 a aya ta 13 zuwa ta 14 da cewa:

***"sa'annan na ji wani mai-tsarki yana magana, wani mai-tsarki dabam kuma ya zantas wa wancan da ke magana, ya ce, har yaushe ne wannan ru'yan nan ta konaniyar hadaya marar-fasawa, da taka shari'a mai-lalataswa, da bada wuri mai-tsarki duk da rundunar yaki garin a tattake su? Ya ce mani, har yamma da safiya guda alfin da dari uku, kana za a tsarkake wuri mai-tsarki."***

Ta wurin wadannan ayoyin mu'a iya ganewa da cewa lamba 3 yana da nasaba ne da nufin Allah, lamba 5 kuma kafara ko kuma fansa, lamba 10 kuma cikawa, lamba 17 kuma samaniya, sa'annan lamba ta 23 shari'a ko kuma hallakaswa.

**<u>LAMBOBI, KAMAR KALAMAI, SUNA BADA LABARAI.</u>**

Kalamai dai-daya suna bamu ma'ana cikin ruhaniya. Sakon da aka bada cikin wata sashen magana yana kara nanatuwa idan lambobin da suke da ma'ana cikin ruhaniya suna samuwa a wannan wurin, ko irin wannan mahallin. Alal misali, mun karanta Korintiyawa ta biyu sura 2 a aya ta 15 da ta 16 cewa;

***"Gama mu shesheki mai-dadi ne na Kristi zuwa ga Allah, cikin wadanda ake cetonsu, da kuma cikin wadanda ke lalacewa; ga wadannan shesheki daga mutuwa zuwa mutuwa, ga wadancan daga rai zuwa rai. Wanene kuwa ya isa wadannan al'amura?"***

Cikin wadannan ayoyi biyu Allah yana kwatanta aikin bishara (wanda shi ne dokar Allah) akan rayuwar wadanda sun saurara. Zai aika canji daya cikin biyu. Allah zai more shi ya kawo rai madawwami da kuma Samaniya ga mai sauraro. Ko kuma, zai kawo fushin Allah domin mai sauraron maganar Allah ya cigaba da tayarwa da dokar Allah.

Abin sha'awa kuma, wannan sakon bishara mai kawo ceto ko shari'a an boye ta cikin dukan



shekarun da ikkilisiyai sun aikadda bishara zuwa cikin duniya. Mun koya cewa lokacin tazarar ikkilisiya ya fara dab da kwatancin Almasihu, a lokacin giciye, yadda ya sha wahala ya kuma mutu domin ya biya hakkin zunubi. Wannan ya kasance cikin shekara ta allip 33. Mun rigaya kuma mun koya da cewa lokacin tazarar ikkilisiya ya fara ne, bisa kaida, akan ranan fentikos, wato 22 ga Mayu, allip 33. Ya kuma cigaba har daidai shekaru 1,955 har zuwa ranar 21 ga Mayu, 1988 lokacin da tazarar ikkilisiya ta kai ga karshe. Lambar 1,955 yana kunshe da lambobi uku masu muhimmanci, wanda kowane a cikinsu yana dauke da ma'ana cikin ruhaniya. Lambobin su ne 5 sau 17 sau 23 = 1,955. Don haka, ta wurin wadannan lambobi Allah yana sanar da wani sako ne cikin ruhaniya da aka furta cikin Korintiyawa ta biyu sura 2 a aya ta 15 zuwa ta 16, wanda an yanke dazu; lamba 5 (kafara ko fansa), lamba 17 (samaniya), lamba 23 (fushin Allah ko hallakaswa).

Babbar kwatancin na biyu yana cikin Yohanna sura 21. Cikin wannan wurin, manzanni sun kama kifaye 153 cikin taru da bai kece ba, da kuma an yi nasara da jan ta har kasa. Za a iya nuna cewa wadannan kifayen 153 suna misalin dukan wadanda sun sami ceto lokacin girbi na karshe na masu bi na gaske da ke aukuwa cikin kwanaki 6,100 na karshe na lokacin matsananciyar kunci. Abin mamaki kuma, tarun bai kece ba, wanda a cikin ruhaniya yana nuna cewa babu masu bi na karya da suke ciki. Wadannan kifayen suna misalin masu bi na gaske ne kadai. Sune taron mai girma na mutane da aka ceta bayan karshen tazarar ikkilisiya, wanda yake gabanai da ranar shari'a. Don haka, nufin Allah ne cewa an tabbatar wa kowa akan ya karbi karashin aikin cetonsa (wato shigo da su samaniya).

Lambar nan 153 yana kunshe da lambobi uku masu muhimmanci, 3 sau 3 sau 17 = 157. Wadannan lambobin suna kwatanta cewa nufin Allah ne (3) ya kawo cikin samaniya (17) wadanda ya ceta cikin kwanakin karshe na lokaci matsananciyar kunci. An maimaita lamba 3 (nufin Allah) domin a nuna cewa abin fa Allah ne ya kafa, kuma ba da jimawa ba Allah ya sa ta auku (duba Farawa sur 41 a aya ta 32). Don haka mun gan yadda cikin ruhaniya Allah yana mara wa kalamai baya da lambobi, wadanda suna samuwa cikin wuri daya ko cikin irin wannan mahallin.

**<u>ME ZAACE DA LAMBAR NAN 722,500?</u>**

Bari mu koma yanzu ga kwanaki 722,5000, wanda suke daga ranar farko da Aprilu, allip 33 (ranar da aka giciye Almasihu, ya kuma mutu) zuwa ranar 21



ga Mayu, shekara ta 2011 (ranar da shirin Allah na ceto zai kamalla duka sa'annan a a chabke dukan masu bi na gaske, ko kuma a fyauce su, zuwa cikin sama).

Lambar nan 722,500 yana kunshe da irin lambobi guda, kashi biyu, lambobi masu muhimmanci kuma. Kowane lamba yana da alaka sosai da shirin Allah na ceto.

<u>5 sau 10 sau 17</u> sau <u>5 sau 10 sau 17</u> = 722,500.

Kwatanci <u>kafara</u> ko kuma <u>fansa</u> ta wurin wahalar da mutuwar Almasihu akan ranar farko ga Aprilu, allip 33 (lamba ta biyar ke nan) zai <u>kamala</u> dari-bisa-dari akan ranar 21 ga Mayu, 2011 (lamba ta 10 ke nan) a sa'anda za a <u>fyauce dukan masu bi na gaske zuwa cikin sama</u> (lamba ta 17). Abin lura kuwa ita ce, an maimaita jerin wannan lamba domin a nuna cewa abin fa Allah ne ya kafa ta zai kuma sa ta auku ba da jimawa ba. (Farawa sura 41 a aya ta 32).

Kaunataccen mai-karatu, ya kamata gaba daya abin da mun koya yanzu ya bamu mamaki. Dukan abubuwan nan da mun koya su'a zama gaskiya ne kadai domin shi Allahn da ya hallici duniya shi ne Allahn da ya shirya daidai jerin lokuta cikin tarihi. Kamar ma yadda dokokin jiki da suke yarda a aikadda roka zuwa cikin Maris, tauraro mai kewaya ranar nan gaba daya, za a iya dogarawa akansu akan gaskiya suke, ko kuma dokokin da suke kewaye da dukan sifar hallita yadda suma gaskiya ne ana kuma iya dogarawa da su, haka ma dokokin da suke kewaye da budewar jerin lokuta na Allah.

Dole mu kara magana akan sifar shaidan nan mai ban mamaki wanda gaba daya akan sakonai Littafi mai Tsarki ya ke jingine.

1. Ranar farko ga Aprilu, allip 33 ita ce ranar da Allah ya jawo hankalinmu, kuma ita ce ranar da aka giciye Almasihu domin a kwatanta yadda ya mutu domin kafarar zunubanmu. Allah yana moran lamba ta 5 domin ya kafa ido akan ranar, har dai idan cikin ruhaniya zata iya nuna kafara.

2. Za a kamala cetonmu gaba daya a lokacin da masu bi na gaske sun karbi tasaassu jikunansu, da za su rayu har-abada. Abin da zai faru akan ranar fyaucewa ke nan, ranar 21 ga Mayu, 2011. Don haka, daga ranar farko ga Aprilu, allip 33 zuwa ranar 21 ga Mayu, 2011 (a hade) ita ce cikaken lokacin daga lokacin da Allah ya nuna mana yadda aka kamala cetonmu zuwa lokacin da cetonmu zata zama cikakiya. Wannan yana daidaituwa sosai da lamba 10, wanda ta ke nuna cikawa.



3. Aka ranar 21 ga Mayu, 2011, ranar fyaucewa, kowane da aka ceta za tafi sama domin an kamala cetonsa gaba daya. Lambar nan 17 ya daidaitu da wannan sosai, domin idan har yana da ma'ana cikin ruhaniya, to samaniya ya ke nunawa.

4. Maimaitawan lambobin nan 5 sau 10 sau 17 kamar maimaitawan wannan sashin magana, "rana daya kamar shekara dubu ne" yana tabbatar mana da cewa Allah ne ya kafa gaskiyar wadannan shaidun, kuma ba da jimawa ba Allah zai sa wannan ya auku. Ko wannan ba abin mamaki bane yadda Allah yake moran wannan kaida na maimaita abu domin ya kara tabbatarwa cewa ranar nan ta 21 ga Mayu, 2011 lallai tabbataciya ce, kamar ma yadda Allah ya more kaidan maimaita abu domin ya tabbatar mana da cewa lallai ranar shari'a daidai take da shekaru 7,000 bayan ruwan tufanan kwanakin Nuhu.

Lallai kam, a fuskar dukan wadannan sakonai masu ban mamaki , ta yaya wani zai yi yunkuri kin yarda da Littafi mai Tsarki game da asalin gaskiyar da ke cewa farawa ranar shari'a da kuma fyaucewa zasu auku akan rana ta 21 ga Mayu, 2011.

Domin karin sakonai akan wannan batu, za ka iya tuntubi Family Stations, Inc., domin samun littatafan nan kyauta.

Littatafai: **"Muna Dab Da Can"** wato "We Are Almost There."
**"Daukaka ya Tabbata ga Allah"** wato "To God be the Glory."
**"Ina Fata Allah zai Cece Ni"** wato "I Hope God Will Save Me."

Kankananan littatafai:
**"Ranar Shari'a: 21 ga Mayu, 2011"** wato "Judgment Day: May 21, 2011."
**"Babu Mutumin Da Ya San Ranar ko Sa'ar" wato** "No Man Knows the Day or The Hour."

Wannan ya kamala karatun mu na wannan yar littafin. Allah ya sa, cikin addu'a ka dubi abin da Allah zai yi da rayuwarka cikin kankani lokaci nan da ya yi saura wa duniyan nan duban abin da ka saurara yanzu.

Yanar gizo: **http://www.familyradio.com**

Addareshi akan gizo:
**international@familyradio.com**

Addareshi gidan-waya:
**Family Stations, Inc.,**
**Oakland, California, 94621, USA.**

RAPTURE/HAUSA 06-29-'10